LAHADI

Don Allah Da Kishin Kasa

# LEADERSHIP A YAU

24.09.17
24 Ga Satumba, 2017
(3 Ga Muharram, 1439)

www.leadershipayau.com

JARIDAR HAUSA MAI FITOWA KULLUM TA FARKO A NIJERIYA

Leadership A Yau LeadershipAyau

No: 002 N150

**Rahoto: Yadda Al'ummar Mahaifar Kwamishinan Ruwan Jihar Gombe Ke Shan Ruwan Kududdufi** > Shafi na 29

**Darewar Gandujiyya Za Ta Kawo Wa APC Cikas — *Sanata Hanga*** > Shafi na 7



## Tun Sani Ɗanƙwairo Ba A Sake Samun Kamar Lil Ameer A Ƙasar Hausa Ba — *Farfesa Abdalla*

*Marigayi LIL AMEER fasihin ƙaramin yaro ne wanda ya taso da matuƙar basira da fiɗce a harkar waƙa, wacce ta shafe yawancin basirar wacce a ka saba gani a ƙasar Hausa ga ƙananan mawaƙa, to amma ashe ba mai tsawon rai ba ne; Lil ya yi rasuwa ta ɓakatatan a ranar 14 ga Satumba, 2017, ya na shekaru 14 ƙacal; lamarin da ya gigita al'ummar ƙasar Hausa, musamman mata da matasa.*

*FARFESA ABDALLA UBA ADAMU ba ɓoyayye ba ne a Arewacin Nijeriya da ma ƙasashen waje, domin ya ƙasance tamkar rumbun ɗakin karatu (library) mafi girma da a ka taɓa yi a ƙasar Hausa, musamman a fannin nazari da binciken nishaɗi a hausance. Kafin*

> Shafi na 2

# Me Komawar Buhari Landon Ke Nufi?

> Shafi na 4



•Shugaban Nijeriya Muhammadu Buhari ya na gaisawa da Shugaba Amurk Donald Trump a birnin New York lokacin taron Majalisar Dinkin Duniya da ya gabata

Abin Jiya Ya Dawo:

## Mahara Sun Kashe Kwamandan Kare Haɗurra, Sun Yi Awon Gaba Da Daya A Zamfara

- *Yarjejeniyar Daina Kisa Mu Ka Cimma Ba Ta Garkuwa Ba, In Ji Su*

Daga **Hussaini Baba**, Gusau

Abin jiya ya dawo jihar Zamfara, inda a ranar Alhamis da misalin ƙarfe tara na safe ne gungun mahara su ka kai hari ofishin Hukumar Kare Haɗura ta Kasa da ke ƙaramar hukumar Tsafe cikin jihar Zamfara su ka harbi rot kwamanda mai suna Mubarak Hamza, wanda nan take ya ce ga garin ku nan, kuma su kai awon gaba da abokin aikinsa mai suna Muhammad Muhammad Birnin Kudu su ka shiga daji da shi.

Bugu da ƙari, maharan sun shaida wa dangin wasu matan Fulani da a ka kama cewa, ba a yi yarjejeniyar daina kama mutane tsakaninsu da jami'ai ba, illa dai an

> Shafi na 8

**Radiyon Biyafara: Laifin Nijeriya Ne, Cewar Ingila** > Shafi na 8

**"Noma Tushen Arziki Ne"** > Shafi na 24

# Tattaunawa

## TA MUSAMMAN

# Tun Sani Ɗanƙwairo Ba A Sake Samun Kamar Lil Ameer A Kasar Hausa Ba — *Farfesa Abdalla*

*rasuwar Lil Ameer a na kallon Farfesa Abdalla a matsayin wanda shi ne mujazar tallata wannan fasihin yaro, domin Farfesa Adamu ba ɓoyayye ba ne wajen taimaka wa matasa masu fasaha irin Ameer.*

*Editanmu NASIR S. GWANGWAZO ya tuntuɓi shehin malamin jami'ar, wanda kuma shi ne mataimakin shugaban jami'a mai cikakken iko ta Nijeriya da ke yanar gizo (NOUN), don jin ta bakinsa kan wannan babbar asara da ƙasar Hausa ta tafka. Duk da irin ɗimbin hidindimun da ke gaban Farfesa Abdalla bai yi ƙasa a gwiwa ba wajen bayar da wasu cikakkun bayanai, waɗanda ba a taɓa jin su a kan rayuwar Lil Ameer ba. Babban abin mamaki shi ne har Lil ya rasu ba su taɓa haɗuwa ido-da-ido da Farfesa ba, duk kuwa da irin ɗimbin gudunmawar da ya ke bai wa rayuwar yaron, wanda hakan ke nuni da irin sadaukarwar Malam Abdalla ga cigaban harshen Hausa. Ga yadda tattaunawar ta kasance:*

**Mai girma Farfesa, shin mene ne cikakken sunan wannan mashahurin yaron mawaƙi da ya rasu, kuma da wane suna ya ke amfani a fagen waƙa?**

Cikakken sunansa Amir Hassan Isa Bello Dambatta. Amma an fi sanin sa da 'Lil A', sunan da shi kansa ya laƙaba wa kansa ko kuma 'Lil Ameer' (mai nufin Amir ɗan ƙarami), a matsayin sunansa na mawaƙi, kamar yadda sauran manyan mawaƙan Rap na Amurka ke yi, misali Dwayne Michael Carter, Jr, wanda a ka fi sani da Lil' Wayne.

**Ta ya ya labarin rasuwarsa ya riske ka, kuma mene ne sanadin rasuwarsa?**

Hassan M. Sheriff na Radio Freedom shi ya fara kira na ranar da abin ya faru, watau Alhamis 14 ga Satumba da yamma ya sanar da ne cewa 'Allah Ya yi wa ɗan gidan ka rasuwa'. Na ce'ai suna da yawa, wannene daga cikin su?' Ya ce 'Lil Ameer'. Wannan sanarwa ta girgiza ni matuƙa, domin ranar ma kasa ci gaba na yin da 'yan aikace-aikacen da na ke yi na rubutu, domin sai na ji duk na rasa ma abin da zan yi, Ina cike da ɗimautuwa. A na ce ma sa 'Ɗan gidan Baba Furof', saboda yadda na ke tallata shi a duniya da kuma begen waƙoƙinsa. Na so in haɗu da shi, domin ganin yadda zan taimaka wajen bunƙasa sha'awar sa ta waƙa, tare da la'akari da cewa shi ɗan sakandare ne, saboda haka akwai buƙatar ya mayar da hankali sosai wajen karatun sa. Allahu Akbar. Allah Ya jiƙan sa da Rahama. Allah Ya ba mu dangana da haƙurin rashin wannan yaro fasihi. Mun buga ta'azziyar sa a http://www.afropop.org/39156/lil-ameer-a-nigerian-rap-prodigy-leaɓes-us-too-soon/

Daga bayanin da ya zo daga baya, sun yi hatsari ne a kan babur. Shi dai an goyo shi ne a kan babur ɗin, sai wani ɗan Adaidaita Sahu, ya yi musu ganganci wajen shige su, wanda haka ta tankaɗa babur ɗin na su ƙarƙashin wata DAF mai tahowa, wacce ta take babur ɗin tare da Ameer ɗin, ta yi sanadiyyar rasuwar sa. Shi mai tuƙa babur ɗin ya rayu amma ya ji rauni sosai. Dan Adaidaita Sahun da aka ce ya janyo hatsarin bai tsaya ba, guduwa ya yi.

> *A yanzu haka, wannan matsayin ya koma kan Dan Bello Ibrahim (Billy-O), Hani Bello Ibrahim, wanda bai wuce shekaru bakwai ba, kuma babban abokin Marigayi Ameer ne (har ma waKar ta'aziyya Hani ya yi wa Ameer) na nan a raye.*

**Mene ne asalinsa da tarihinsa?**

An haife shi 22 ga Mayu 2003, ya kuma rasu 14 ga Satumba 2017. Ya rasu ya na da shekaru 14 da watanni uku da rabi kenan. Mutumin Dambatta ne a Kano, amma a Tarauni da ke cikin birnin Kano su ke da zama.

**Wacce basira ka gani a tattare da shi har ka janyo shi a jikinka?**

Abin mamakin shi ne ba mu taɓa haɗuwa da shi ba, kamar yadda na gaya maka ɗazu, to amma mun san juna kuma muna magana ta waya. A lokacin da na gayyaci waɗansu Amurkawa daga www.afropop.org su zo su yi shiri na musamman a kan Hausa Rap a farkon Fabairu 2017, Ameer na ɗaya daga cikin mawaƙan da na ce lallai sai sun yi hira da shi saboda tallata shi a duniya.

**A ganinka, me ya sa rasuwarsa ta ɗauki hankalin jama'a?**

Dalilai guda biyu. Na farko ƙarancin shekarun sa – mutuwar yara razanawa ce da ita fiye da mutuwar manya. Na biyu basirar sa. A ɗanɗankanin lokaci Allah Ya sa sunan sa ya bazu ko'ina, ta yadda sai gayyatar sa a ke yi ya zo ya yi wasa a garuruwa da dama.

**Ko Malam ya san yadda dangantakar yaron ta ke da mahaifiyarsa?**

Dangantakar sa da mahaifiyar sa ba za ta misalu ba, don shi ne ma wanda ta fi shaɗuwa da shi a cikin 'ya'yanta.

**Su nawa ne a ɗakinsu da gidansu, kuma ɗa na nawa ne shi?**

Su shida ne a ɗakinsu, amman shine na uku.

**A wane hali yanzu iyayensa da 'yan uwansa ke ciki a dalilin rasuwar?**

Su na cikin ɗimautuwa da damuwa, kamar yadda kowacce mutuwa ke kawo wa, ballantana ta ɗan ƙaramin yaro kuma ba zato ba tsammani.



•Yerima Usman Shettima

**Shin ya na taimakon iyayensa da abinda ya ke samu daga waƙa, kafin rasuwarsa?**

Ai yanzu ya fara, domin ko faifan farko ma bai saki ba tukunna, duk da ya yi waƙoƙi kamar 20. Ya na kan gwaji ne na waƙokinsa da kuma ƙarbuwarsu, wanda dama sai an yi haka sosai sannan a saki CD na waƙoƙin da suka fi karɓuwa. Saboda haka kuɗin ba su fara samuwa sosai ba, amman dai ya na da tausayin mahaifiyarsa da 'yan uwansa.

Ci gaba daga shafi na 6



Michael Jackson yana ɗan ƙaramin yaro yana waƙa

# ‘Tun Sani Ɗankwairo Ba A Sake Samun Kamar Lil Ameer A Ƙasar Hausa Ba’

> Ci gaba a shafi na 2

Sannan mahaifiyar sa ita ce ta fara zama manaja ɗin sa kafin Abba Usman (Abba PA) ya karɓi ragamar abin. Kuma a gaskiya ta kashe kuɗaɗe da dama a kan harkarsa kafin Allah Ya yi ma sa rasuwa.

**Shin ko Malam ya san babban burin yaron, kafin ya rasu?**

Burinsa ya zama matuƙin jirgin sama, watau Pilot, duk da cewa ya na sha’awar waƙa.

**Wacce asara ka ke ganin al’umma ta yi a dalilin rasuwarsa da ma matasa masu basira irinsa?**

Babbar asarar ita ce rashin yaro mai ƙananan shekaru mai kuma fasaharsa da ƙwarewarsa wajen sarrafa waƙa. Tun bayan mutuwar Alhaji Sani Zaƙin Murya na Dankwairo, ba na jin an samu wani ƙaramin yaro da ya kama ƙafar Ameer wajen sarrafa waƙa da kuma rashin nuna tsoron barazanar jama’a in ya hau dandali don yi waƙa. Shigowarsa cikin sana’ar waƙa ta rufe wani giɗi na nishaɗin ƙananan yara a ƙasar Hausa, wanda kuma kamar yadda jama’a da dama za su iya sani, waɗansu daga cikin mashahuran mawaƙan duniya sun fara ne tun su na ƙananan yara. Babban misali shi ne Marigayi Michael Jackson wanda ya fara waƙa ne tun ya na ɗan shekara biyar.

Haka ma Kris Kross, yara guda biyu, Chris “Mac Daddy” Kelly da Chris “Daddy Mac” Smith, waɗanda su ka shahara da waƙar Rap mai suna ‘Jump Jump’ sun yi suna ne tun su na ’yan shekaru 12.

A yanzu haka, wannan matsayin ya koma kan Dan Bello Ibrahim (Billy-O), Hani Bello Ibrahim, wanda bai wuce shekaru bakwai ba, kuma babban abokin Marigayi Ameer ne (har ma waKar ta’aziyya Hani ya yi wa Ameer) da nan a raye. Da fatan zai maye gurbin Ameer ɗin.

**Akwai masu ra’ayin cewa, rasuwar yaron nan ta fi alheri, saboda gudun kada ya zama hatsabibi, idan da ya yi tsawon rai. Me Malam zai ce kan hakan?**

Wannan ba daidai ba ne, domin duk Musulmin duniya zai yi wa rasuwar wani Musulmin addu’a ne. Kamata ya yi masu wannan ra’ayin su ma su yi fatan mutuwa yanzu-yanzu, domin babu tabbacin za su ɗare duniyar da imanin da su ke ganin su na da shi. Saboda haka yaya za su yi hasashen makomar wani?

Sannan kuma Ameer da sani da kuma albarkacin iyayensa ya shiga sana’ar waƙa – ta wannan ma ai ya samu kariya duniya da lahira daga sharrin shaiɗan da rundunarsa. Bayan haka, mu da mu ke mara masa baya, ta kowacce hanya, ai mun ɗauke shi tamkar ɗan da mu ka haifa, kuma da namu ’ya’yan, waɗansu su na waƙa (kamar ɗan Billy-O da na yi magana). Ta ɗaɗa za mu ƙyale ya lalace bayan amana ya ke a wurinmu? Wannan ba wani abu ba ne illa ɗyashi da hassada, saboda yaron ya sami ɗaukaka saboda basirar da Allah Ya yi ma sa.

**Malam, kai kanka da a ke ganin ka yi fice a sha’anin haɗaka harshen Hausa, wasu na ganin cewa, ka na rusa yaren da al’adunsa, saboda taimakawa irin waɗannan yara masu waƙar gambarar zamani (wato hip-hop) da ka ke yi. Me za ka ce kan hakan?**



•Marigayi Ameer a sutudiyo

Bari in kawar da wata mummunar fassara tun kafin a yi nisa. Hiphop da Rap ba gambara ba ne. Ko kaɗan. Wanda duk ya ke faɗin haka, to ko da ya san gambara, bai san Hip Hop ba. Jigon gambara akasari batsa, zambo, zolaya, shakiyanci, ban dariya da sauransu. Ko kaɗan waɗannan ba sa cikin abin da Rapawa ke rerawa, takamaimai ma na mu na ƙasar Hausa.

Hip Hop salo ne na rayuwar matasa ta shigar su ta tufafi. Rap salo ne na waƙar matasa, kuma duk waɗannan daga Amurka a ka samo asalin sigarsu ta yanzu. Mutum zai iya zama mawaƙin Rap, amma ba ɗan Hip Hop ba (misali DMD), kuma ba duk masu ra’ayin Hip Hop ne ke waƙar ba. Rap salo ne na harbo furuci a jere, domin nuna gwanintar jera kalmomi su dace da jigon waƙar, wanda mu a nan ƙasar Hausa, akasari a kan ilimi ne, rayuwar duniya, nasiha, da kuma kamfama kai, watau zuga kai.



•Marigayi Ameer a sutudiyo

A ƙasar Hausa akwai masu Rap tun kafin na zamani ya shigo. Waɗannan sun haɗa da Bagobiri Sullutu da kuma Madawakin Maganana Sarkin Zazzau. A Hausance, waɗannan mawaƙan ba za a kira su ’yan gambara ba. Na ke jin danganta Rap da gambara ya samo asali tun lokacin da Billy-O ya yi wani chalikanci a waƙarsa ta ‘Ban Tubani’. Waɗanda ba su san me a ke nufi da Rap ba sai su ka ɗauka ai indai irin yadda Billy O ke yi ne, to gambara ce, wanda haka kuma babban kuskure ne, domin ba su yi bincike sun gane me a ke nufi da Hip hop ba.

Sannan duk wanda ka ga ya lalace, to da ma can lalatacce ne, babu ruwan hanyoyin sadarwa da lalacewarsa. An sha tafka wannan muhawarar. Su masu nishaɗin hululu gani su ke Ina yi mu su hassada (baran ma ’yan fim) in na janyo hankali a kan al’adu; su kuma mutanen gari gani su ke Ina goyon bayan rusa al’ada. Kullum a wannan tsaka mai wuyar na ke. Har yanzu ba na jin akwai wani mai sana’ar nishadin Hausa guda ɗaya tak da ya taba zama ya karanta abubuwan da na ke rubutawa a kan sana’ar, kuma duk na saka su kyauta a gani a www.auadamu.com.

Na sha faɗar cewa ni aiki na, nazari, ba yanke hukunci ba. Duk abin da mutum ya yi zan nazarce shi, ko mai kyau ne ko marar kyau ne – kuma ba zan nuna kyau ko akasin haka ba a abin da mutum ya ke yi, saboda haka ingantancen nazari ya gada: dole manazarci ya cire kansa daga cikin nazarin, ya bayar da bayanin da ya gani bisa doron manhajar tubulin famihta (watau theoretical framework).

**Shin ya ka ke hasashen zai zama makomar waƙoƙin da a ka fi sani, kafin na gambarar Hausa nan gaba, idan wannan hip-hop ya yi cigaba da bunƙasa?**

Waɗanne ne ‘a ka fi sani’? Ka na nufin na gargajiya? Babu wani yunƙurin da mu ke yi na raya su. Kullum sanannun dai su a ke ta juyawa – Shata, Dankwaro, Danmaraya, Sani Sabulu, Dandawo da sauransu. Waɗannan ingantattun mawaƙa ne. Amma wane yunƙuri a ke yi domin samar da matasa mawaƙa irinsu? Ni kaina na fitar da kuɗi na saki album na waƙoƙin Nasiru Garba Supa, watau ɗan Marigayi Alhaji Garba Supa, kuma tare da Nasiru mu ka shiga sutudiyo mu ka yi sati guda mu na ɗaukar waƙoƙin, a ka tace a ka bi duk ƙa’idojin sakin album, a ka sake shi. Amma bai yi kasuwa ba. A Turai, za ka ga a na raya na da, da kuma na yanzu. Misali, yau shekarar Ludwig ɓon Beethoɓen, mai rubuta kidan classical, kuma mutumin Bonn, Jamus, 190 da rasuwa. Amma har yanzu a na raya kiɗansa, kuma wannan bai gushe sababbin makaƙan classical kamar su Dobrinka Tabakoɓa, Missy Mazzoli, Judd Greenstein da Ann Cleare da sauransu. Rap dai ya iso, kuma zai rayu. Kazalika kiɗan gargajiya – in halin-ko-in-kula bai kashe shi ba, domin ɗaya bayan ɗaya, duk waɗanda a ka sani sun riga mu gidan gaskiya. In ba a samu madadinsu ba, to wata rana shi ma kiɗan zan tsaya cak.

Mun gode. Allah Ya saka da alheri. Bissalam!

Madalla.